*Bijochs: Dec, 2025 Vol. 3 - Issue, 2 ID No. 013 (Pg. 144-155)*

# Garin Na Ji Daɗi: Tsokaci Kan Tattalin Arzikin Hausawan Garin Gombi Jihar Adamawa, Jiya da Yau

**Isa Umar Al-Musawi**
isaumaralmusawi@gmail.com
+2347037131666
Sashen Nazarin Harshen Hausa
Kwalejin Ilimi ta Tarayya, Yola
Jihar Adamawa

***Tsakure***

*Wannan takardar mai taken "Garin Na Ji Daɗi: Tsokaci Kan Tattalin Arzikin Hausawan Garin Gombi Jihar Adamawa, Jiya da Yau" ta bayyana kowane ne Bahaushe a taƙaice, yadda tattalin arzikinsa yake. Sannan ta nuna ƙoƙarin da Bahaushe yake da shi na yawace-yawacen neman halal, domin ya inganta rayuwarsa ta ɓangaren tattalin arziki. Wadda hakan ya kai shi wani wuri da ake cewa Gombi a jihar Adamawa. Ya kuma fafata har ya samu abin buƙata na sha da na wanka. Har ila yau binciken ya ƙyallaro sana'o'i da kasuwanci da ƙwadagon da Hausawa mazansu da matansu da kuma na tarayya suke aiwatarwa. Makasudin binciken bai wuce 'yar masaniyar da mai binciken yake da ita game da harshen Hausa da al'adunsa ba, kuma yana da zama a garin na Gombi, sannan yake da yaƙinin ba za a rasa natijar da garin da al'ummominsa suka samu ta dalilin tattalin arzikin Hausawa ba, wannan shi ya tunzura shi gudanar da binciken. Sannan an ɗora wannan binciken ne bisa ra'in sauye-sauyen tattalin arzikin al'umma (Economical Theory of Social Change).Wanda masanin tsumi da tanadin nan (Karl Marx) ya samar a 1859 (Ado, 2017). Wannan ra'i yana bayani ne game da sauyesauye da yake faruwa ga al'umma ko al'adunsu daga wani matsayi zuwa wani matsayi, kamar yadda Hausawa suka zo garin na Gombi a matsayin baƙi, ta dalilin ƙoƙari suka yi abin kansu. Dangane da hanyoyin da aka bi wurin tattara bayanan binciken kuwa sun haɗa da tattaunawa da masana da kuma sanya idanu ga lamuran da ke kai komo a garin ta fannin tattalin arzikin Hausawa. Daga ƙarshe takardar ta bayyana nasarorin da Hausawa suka samu a sakamakon haƙuri da naci da kuma haɗa ƙarfi da ƙarfe domin cim ma nasara wanda ya sanya haƙarsu ta cim ma ruwa, ta hanyar rayar da wasu daga cikin sana'o'in gargajiya na gadon gidajensu, dangin fatauci da kasuwanci. Sai kuma riƙar wasu nau'i na kasuwanci da 'yan ƙasa ba su fiye yi ba. Musamman arkomin zamani, ga kuma tsayuwar da mata suka yi ta fannin neman halal dangin Ungozoma da ƙunshi da sauran bayar da taimako na gyaran aure (maganin mata). Sun kuma muhimmantar da sana'o'i na tarayya kamar kiwon Kifi da Shanu da Zomo ga kuma noman zamani misalin na rani (Fadama I, II & III).*

**Fitilun Kalmomi:** Gombi, Hausawa, Sana'o'i, Tattalin arziki.

## 1.0 Gabatarwa

Na zaune bai ga gari ba, haka Hausawa suke yi wa mai yawon ganin gari, ko yawon neman halal kirari. Kuma babu maraya sai rago inji masu hikimar magana, shi Bahaushen mutum sananne ne ga kowa wurin neman na kansa, wanda hakan ya sa bayan ya nemi na kansa a ƙasarsa ta

haihuwa, kuma yake niƙar gari ya shuri takalmarsa ya bazama duniya don ya nemi abin masarufi, wanda hakan ke sa ya kashe ƙwarƙwatarsa, ta hanyar samun abin hannu (rufin asiri). Sanin kowa ne Hausawa da yawansu 'yan kasuwa ne, bincike ya tabbatar da cewa Hausawa suna da 'yan kasuwa masu yawa a cikinsu. Tun a zamani mai tsawo sukan yi ciniki a tsakaninsu da al'ummomi… da sauran ƙasashen maƙwabtansu (Ado, 2017 da AlMusawi, 2023). Bahaushe ya daɗe da yawace-yawacen neman kuɗi domin ya bunƙasa nasa tattalin arziƙin, wanda har ya samu isowa wurin da ake cewa Gombi ta jihar Adamawa a yau, wannan wuri (Gombi) ya yi masa daɗi domin ya samu inda ya ɓarje guminsa ya miƙe ƙafafu saboda samun duniya, inda ya yi mata ya yi mota ya yi babban shago da kuma gidan alfarma, sannan yake cin duniyarsa da tsinke, sakamakon jajircewar da ya yi wurin zage dantsen tattala abin da ke hannunsa.

## 1.1 Manufar Bincike

Manufar wannan bincike, ita ce cike giɓin da aka bari a fannin ilmi, tare da bayyanar da wanzuwar Hausawa a garin Gombi. Sannan ya taɓo irin ƙoƙarin da Bahaushe ya yi wurin neman halalinsa a ɓangaren tattalin arziki har ya taimaka wa waninsa.

## 1.2 Bayanin Maƙasudin Bincike

Kasancewar mai binciken yana da 'yar masaniya game da harshen Hausa da al'adunsa, kuma yana da zama a garin na Gombi, yake da yaƙinin ba za a rasa natijar da garin da al'ummominsa suka samu ta dalilin tattalin arzikin Hausawa ba.

## 2.0 Sharhin Ayyukan Magabata

Kalmar tattali tana nufin kula ko ririta ko tanadi da adana wani abu, watau tsiminsa. Ita kuwa kalmar arziki a nan tana nufin tajirci ko dukiya ko samu ko hali ko kuɗi ko sukuni da makamantansu. Daga waɗannan bayyanai za a ga, a ma'ana ta gama gari, tattalin arziki yana nufin kula da dukiya. A fagen nazari kuwa, tsari ne na sarrafa albarkatun ƙasa da sauran ni'imomin da Allah ya yi wa mutane (Umar, 2011).

Wani masani kuwa ya dubi ma'anar tattalin arziki da cewa kula da abin da aka mallaka ko rainonsa ko ririta shi da ba shi kyakkyawar kulawa domin bunƙasa da cin moriyar da ake samu daga wannan abin (Maikwari da Lawan, 2022). Sannan Umar (2011) da Ibrahim (1983), sun bayyana tattalin arziki da cewa tsari ne na sarrafa albarkatun ƙasa da sauran ni'imomin da Allah ya hore wa mutum, domin samar da muhimman abubuwan da ɗan Adam yake buƙata tare da rarraba su ga sauran al'umma. Saboda haka, ala tilas mutum ya yi gwagwarmaya don kai wa ga biyan buƙatunsa na yau da kullum. Ga hakan kuwa, ya zama tilas mutum ya dogara da waninsa kamar yadda wanin nasa yake dogaro da shi saboda a gudu tare a kuma tsira tare, a fannin biɗa da kuma tanadi (Umar, 2011)

Hausawa suna da ƙasa mai yabanya da dausayi, wanda hakan ya taimaka suke tasarrufi da ita wurin bunƙasa tattalin arzikinsu, ta fuskar abubuwan buƙatun ɗan Adam musamman abinci da muhalli da sutura. Daga cikin waɗanda muka lissafa sai mu ga tilas ne ɗan Adam ya yi aiki tuƙuru domin ya sarrafa wasu abubuwa saboda

buƙatunsa. Shi ɗan Adam a tilonsa ba zai iya wadatar da kansa ba, sai da taimakon waninsa. Umar (2011), yana cewa tilas ne mutum ya dogara ko ya jingina da sauran 'yan uwa domin samun wasu abubuwa, kamar yadda su ma suka dogara da shi, wannan ya sa tattalin arziki ya ƙunshi samun abubuwan buƙatu da yadda za a rarraba su tsakanin jama'a da kuma sigar yadda ake amfani da su.

A ƙasar Hausa an tabbatar akwai sana'o'i da yawa waɗanda aka gada a wajen iyaye da kakanni kuma suke rufa wa mutum asiri a wajen samun abinci da sutura da wajen zama da kula da rayuwarsa. Daga cikin sana'o'in Hausawa na gargajiya akwai sana'o'in maza kawai da sana'o'in mata kawai da kuma sana'o'in maza da mata, kamar yadda Gwammaja (2010) ya tabbatar.

### 2.1 Shikashikan Tattalin Arzikin Hausawa

A Bahaushiyar al'ada akwai hanyoyin da Hausawa suka dogara da su a matsayin shikashikan tattalin arzikinsu tun iyaye da kakanni, saboda haka ne ma ya sanya ake ganin waɗannan su ne suka zama ƙashin bayan nema da sarrafawa ga rayuwar kowanne Bahaushe a tilonsa da kuma a jam'ance. Wannan ne ya sanya Auta (2006), yake cewa abubuwa uku su ne suka zama shiƙa-shiƙan tattalin arzikin Hausawa, waɗanda suka haɗa da:

#### 2.1.1 Sana'o'in Gargajiya

Sana'o'i jam'i ne na sana'a, wadda sana'a kuwa tana da ma'anar sarrafa albarkatu da sauran ni'imomin da Allah ya hore wa mutum, na daga dabbobi da tsirrai da kuma ma'adinan ƙasa.Idan mutum ya samu wata hanya ta samun abin biyan buƙata na daga kuɗi ko abinci ko wanin waɗannan, sannan makusantansa suka fahimci hakan, wannan shi ne sana'a (Maikwari da Lawan, 2022). Sannan Abuubaida, Umar & Ibrahim (2019), sun ƙara da cewa kowanne gidan Bahaushe akwai sana'a, wasu gidajen ma sana'o'i da dama ake aiwatarwa kuma kowa yana yin su. Babu wanda yake zaman banza. Waɗannan sana'oin da suka danganci gargajiya da Hausawa suka gada tun iyaye da kakanni suke aiwatarwa a gidajensu, sun haɗa da; Noma da Saƙa da Sassaƙa da Ƙira da Farauta da Su da Bori da Wanzanci da Jima da Dukanci da Fawa da sauransu.

Sannan shi kuwa Durumin Iya (2006), ya bayyana ra'ayinsa game da sana'a da cewa shi ne tafarki karɓaɓɓe ga jama'a da ya jiɓanci haƙuri da juriya da motsa gaɓoɓi da hikima da jari da karakaina domin samun halali. Sana'o'i kamar su sata da karuwanci da daudu (Ɗan daudu) duk sana'o'i ne a ƙasar Hausa, amma ba karɓaɓɓu ba ne a wurin jama'a. Wato dai sana'a hanya ce ta dogaro da kai da tsayuwa da ƙafafu, domin biya wa kai buƙatun da suka shafi ci da sha da sutura da muhalli.

#### 2.1.2 Kasuwaci da Fatauci

Kasuwanci yana nufin saye da sayarwa na daga abin buƙatar yau da kullum ga mabuƙata a lokacin da suke buƙata kuma a wurin da suke buƙatar abin. ko aikata wani aikin da zai samar wa mutum riba wadda zai kore wa bakinsa ƙuda ko mugun yawu (Durumin Iya, 2006).

Su ma waɗannan suna daga cikin hanyoyin bunƙasa tattalin arzikin Hausawa. Wasu ana

saya a sayar ne a wuri guda, wasu kuwa in an saya sai an kai wani wuri ake sayarwa. Su ma sun haɗa da; Atai da Kiri da Jaura da Dillanci da Arkomi da Botori da ‘Yar maiganye da makamantansu.

**2.1.3. Kwadago**

Kwadago yana nan kamar leburanci ne, domin za a yi aiki ne, sannan a biya wahalar, saboda haka yana tattala arziki shi ma. Misalansu sun haɗa da; Yanta da Kitso da Safkale da Gini da Jinka da Dakau da Dako da Gyartai da Niƙau da Wanki da Guga da Faskare da Yankan Farce da waninsu. Sannan ta fuskar sarakuna ko gwamnati kuwa sun haɗa da: Haraji na jama’a da jangali na dabbobi sai kuma tara da akan yi wa mutane domin samun kuɗin shiga (Auta, 2006).

Su ma Bunza (2017) da Ramatu Abdullahi Maiyaki (2022), sun kawo sana’o’in gargajiya da ma sana’o’in da mata suke yi. Kamar haka: Sana’o’in Gargajiya su waɗannan nau'i na sana'o'in, Bahaushe ya gaje su ne tun kafin ya haɗu da wata al'umma, sana'o'in kuwa sun haɗa da; Noma da Kira da Saƙa da Sassaƙa da Kamun Kifi da Wanzanci da Kwadago da Koli da Jaura da Sakai da Awo da Fatauci da Dillanci da Feke da Gyartai da Bugu da Dukanci da Ɗinki. Sana’o’in mata; su kuwa sana'o'i ne da galiban mata zalla suke aiwatar da su, ba a faye samun maza suna aiwatar da su ba, misalan waɗannan sana'o'in sun haɗa da: Kitso da Dafe-dafe da Tayetoye da Saƙe-saƙe da Sussuka da Shiƙa da Reno da Awo da Adashe da Biki da Ga ruwa.

**2.2 Taƙaitaccen Tarihin Hausawa**

Kalmar *Hausa*, kalma ce da take da gaɓa biyu watau ‘*Hau*’ da ‘*Sa’*. Harshe ne na wata jama’a da ke rayuwa a kudancin Hamadar sahara (Al-Musawi, 2016). Duk da cewa masana sun sassaɓa kan yadda aka samo sunan wannan kalmar. Kamar Funtua (2010), yana da ra’ayin kalmar ta samo asali ne daga kalmar Habasha. Shi kuwa Adamu (1997), yana da ra’ayin cewa an samo kalmar Hausa ne daga Buzaye, domin kuwa haka suke kiran mutanen da ke zaune a arewacin kogin Kwara, wato Hausa. Ya kuma ƙara da cewa, harshen Hausa yana ɗaya daga cikin harsuna iyalan Cadi. Hakan bai hana a ce da Hausa shi ne harshen da Hausawa suke magana da shi ba, kamar yadda Hausawa suke amfani da shi ta hanyar magana da mu'amala. Dalilin hakan kuwa, mafi yawan ƙabilu suna kiran Hausawa da sunan Hausa (Adamu 1978, CNHN 1981 da CNHN, 2006). Hausawa mutane ne masu tsananin riƙo da al’adunsu na gargajiya, musanman wajen tufafi da abinci da lamuran da suka shafi aure da haihuwa da mutuwa da sha’anin mu’amala tsakanin dangi da abokai da shugabanni da kuma lamuran sana’a ko kasuwanci ko neman ilimi da sauransu (Adamu, 1997 da Adamu, 2020 da Al-Musawi, 2023). Sannan an bayyana wurin da ƙasar Hausa take da cewa:

> *Farfajiyar da Hausawan asali suka yanke cibi. Makekiyar ƙasa da Hausawa suka mamaye su kaɗai, nan ciki kakanin kakaninsu suka tsira. Nan suka sami kansu, a nan aka same su. Ba su san wata ƙasa ba sai ita. Ba a*

> *san su a ko'ina ba, sai a nan. Ba su yi tarayya da kowa ba. Ba ga kowa suka karɓe ta ba, kuma babu wanda ya yi musu masauki a cikinta. Da ita suke tinƙaho, domin ba su san ko'ina ba bayan ta. Da ita ake yi musu suna da garuruwansu da daulolinsu da zuri'arsu da addininsu da al'adunsu. A doronta suka kakkafa mazauninsu na din-din-din mannanu ƙuda ya faɗa ƙwaryar alewa.*
> (Bunza, 2015).

Hausawa mutane ne baƙaƙe watau baƙar fata, ba farar fata ba, ko da yake akan samu 'yan farare jifa-jifa musamman in aka samu auratayya da wata ƙabila. Dangane da abinci da Bahaushe yake mu'amala da shi kuwa a matsayin cimaka Adamu (1997), ya bayyana cewa:

> *Yawancin abincin Bahaushe kuwa ana yin sa ne da gero ko dawa ko maiwa. Sai kuma sauran abubuwan haɗawa albasa, kuka, kuɓewa, tafarnuwa, karkashi, lalo, tafasa, da ɗata. Sai kuma kaya irin na marmari, kamar su wake da shinkafa da acca, da ibiro da kuma kayan rafi, da sauran ire-irensu.*

Dangane da addininsu kuwa yawancin Hausawa musulmai ne, saboda haka mafi yawan al'adun da suka shafi aure da haihuwa da mutuwa da sauran hidimomin yau duk sun dogara ne ta yadda addinin ya nuna, kodayake akan samu Hausawa masu bin addinin Kiristanci, hakan ma bai hana a samu masu bin addinin gargajiya dangin Maguzanci da wanin waɗannan ba (Ibrahim, 1982 da Al-Musawi, 2023).

Dangane da zaman iyali Bunza (2015), ya bayyana cewa Hausawa suna da tsarin zaman gandu ne a ɓangaren iyali, a gida ɗaya ana samun kaka da uba da 'ya'ya da jikoki har ma da tattaɓa kunne. Wannan shi ya ba da damar cuɗeni-in-cuɗe-ka, tare da tsarin taimaka wa juna. Haka nan akan samu mutuntawa da girmamawa tsakanin talaka da saraki, haka tsakanin malami da ɗalibi, tsakanin mawadaci da mabuƙaci ma hakan abin yake.

### 2.3 Garin Gombi

Gombi gari ne da ke kan tudu ta ko'ina in za a shige shi, cikin garin yana da shimfiɗaɗɗun layuka gwanin ban sha'awa. Sannan dazukansa suna da yabanya mai kyau da kyau domin noma. Shi ne cibiyar ƙaramar hukumar Gombi, sannan a cikin garin ne matsugunin (fada) hakimin gundumar Guyaku yake. Akwai dagatai guda biyu (Gombi Asali da Gombi Fulani) tare da mazaɓu biyu (Gombi North da Gombi Sourth) a siyasance. Yana da yawan jama'ar da suka kai mutum dubu ɗari da arba'in da bakwai da ɗarin bakwai da tamanin da bakwai (147,787) bisa ƙidayar shekarar 2006.Yana da faɗin kadada dubu ɗaya da ɗari ɗaya da ɗaya (1,101) na murabba'in kilomita. Yana kuma da nisan kilomita ɗari da goma sha biyar (115) zuwa fadar jihar Adamawa (Yola).

Sannan garin ya haɗa iyakoki da ƙanannan hukumomin Hong ta Gabas da Hawul (Borno) ta Arewa da Shani (Borno) ta

Arewa maso Yamma sai Shelleng ta Yamma maso Kudu sai kuma Song ta Kudancinsa. Saboda haka yana nan a layi na goma ($10^0$N) a Arewa da kuma layi na goma sha biyu ($12^0$E) Gabas da ikwaita.

Ƙabilun da ke zaune a wurin sun haɗa da Gwaba da Hona da Bura da Lala da Ga'anda da Fulani da Kilba da Margi da Kanuri… sai kuma kanwa uwar gami wato Hausa. Sana'o'in da suka fi bayyana ga kowa kuma abin tasrifi babu kamar Noma da kiwo sai kuma kasuwanci, waɗanda su ne suka fi jan hankalin baƙi daga wurare dabandaban zuwa garin (Vanguard Yellow pages, 1988). Haka nan garin Gombi yana nan tun kafin 1940[1], sai dai babu wata jama'a mai yawa a wurin in ka cire Fulani makiyaya, sai dai a gefen wurin akwai wasu ƙabilu kamar Hona da Gwaba a wurin da ake ce da shi Balda[2], a yadda binciken ya gano. Gombi bai samu ba, sai dalilin samar da hanyar da ta taso daga garin Biu ta biyo ta garin Garkiɗa ta iso wurin da ake cewa Gombi a yau, ta bi ta garin Song ta yi birnin Yola a shekarar 1943 (AlMusawi, 2023).

**2.4 Zuwan Hausawa Garin Gombi.**

Sanin kowa ne Bahaushe mutum ne mai yawon neman na kansa wanda ya kasance mai kazar-kazar wurin neman halal. Hakan shi ya sanya bayan neman na kansa a gida (ƙasar Hausa) yakan kuma fita maƙwabta domin tsira da mutuncinsa. A hakan ne Hausawa wurin yawace-yawacensu, suka isa garin da ake cewa Gombi a yankin Adamawa na yau. Binciken ya gano cewa Hausawa sun iso wurin da ake ce wa Gombi ne a wuraren shekarar 1939, sannan ya kuma gano cewa kafin sunan Gombi ya bayyana ana ce da wurin *Sangere Mbororo* (mararrabar Fulani) ko kuma *Gobare* (takin dabbobi), saboda Fulani ne a wurin[3]. Sannan AlMusawi, (2023), ya ƙara da cewa ko da yake wasu suna da ra'ayin cewa sunan Gombi ya samu ne da harshen Fulatanci '*Kombi*' (kusa) wato *Kombi lawol* (kusa da hanya). Ko ma dai mene ne, Gombi ya samu sunansa kuma yana amsa wannan sunan.

Zuwan Hausawan farko, Hausawa ba sun zo Gombi a take gaba ɗayansu ba ne, a'a sun zo ne da kaɗan-kaɗan. Hausawan da suka fara zuwa Gombi sanannu sun haɗa da: Alhaji Zango mai fata da Malam Musa Maibaƙin jini da Alhaji Adamu Manjahota da Alhaji Adamu mai Kanwa da Malam Ibrahim Ɗan'iya da Malam Ahmadu Girei da Malam Ahmadu mai dogon Jaki da Malam Shehu mai kanwa da Malam Mai Tarko. Waɗannan Hausawa kasuwanci ya kawo su, daga masu sayan ƙiraga (fatu) sai 'yan koli da masu kanwa da tabarmi, a bisa bayanan da muka samu[4]. Malam Babba da Malam Yakubu Gaya da Alaramma Malam Salisu da wasunsu. Kamar yadda binciken ya tabbatar cewa wasu ma tsangaya suka kafa[5].

---

1. Alh. Musa Ibrahim (66) masanin Guyaku, kuma shugaban Majalisar Musulmi (Muslim Council Gombi), an yi hira da shi (8:108:48pm) ranar 13/09/2019 a gidansa da ke Unguwar T/Margi, Gombi.

2. Alh. Muhammadu Yuguda Toɓi (67) Tela ne, an yi hira da shi (9:169:39am) a rumfarsa ranar 14/09/2019 a Tsohuwar kasuwa, Gombi.

3. Mal. Muhammadu Witi (93) mai hayar keke an yi hira da shi (11:00am11:30am) ranar 14/09/2019 a ƙofar Mal. Arabiya, Gombi.

4. Alh. Yusuf Ahmad Arabi (maikanti) (80) tsohon mai kuɗi an yi hira da shi (9:00am9:58am) a ranar

14/09/2019 a ƙofar gidansa da ke unguwar faransa, Gombi.

5. Alh. Abubakar Usman (60) Ɗan kwangila ne an yi hira da shi (7:10am-8:55) ranar 15/09/2019 a gidansa da ke kasuwar butu, Gombi.

A karo na biyu kuwa Hausawan sun zo Gombi ne a kan hanyarsu ta zuwa aikin Hajji daga ƙasar Hausa, kasancewar garin Gombi yana yankin Arewa maso gabas ne daga ƙasar Hausa. Hakan ta sanya wasu sukan ya da zango suka ci gaba da zama, yayinda wasu kuwa sukan wuce zuwa aikin Hajji, waɗannan Hausawan waɗanda suka zauna su ne: Alaramma Rukuni na uku kuwa wannan rukuni na Hausawa yawancinsu sun zo ne dalilin noma saboda an yi fari a wurin da suke na asali. Wasu kuwa saboda an tashe su a filin da suke noma, domin za a yi kamfanin Tumatur, a Dadin Kowa (Gombe). Ko da yake an samu wasu malamai daga cikin wannan rukunin. Waɗannan su ne: Alaramma Ɗan'amus da Malam Garba mai Shayi da Malam Nomau sarkin Hausawa da Malam Buba Dadin Kowa, da sauransu. Binciken ya bayyana faruwar hakan a wuraren shekarar 1973 (AlMusawi, 2022).

To, daga waɗancan rukunan Hausawan farko da na biyu da na uku, sai waɗanda suka zo daga baya wato daga shekarar 1978. Kuma su kansu akwai dalilai mabambanta da ya kawo su, wasu malamai ne, wasu 'yan kasuwa ne, wasu manoma ne, wasu kuwa 'yan ci rani ne. Wannan rukunin Hausawa kuwa ya ƙunshi: Alaramma Buba Basulluɓe da Alaramma Ɗan'amus da Malam Sani mai Kwanuka da Malam Ahmadu Bahaɗeje da sauransu, kamar yadda bincikenmu ya gano[6]. Kuma daga wannan rukuni har zuwa yau za a sanya shi a rukunin ƙarshe, saboda jama'a ta yi yawa ba ka sanin lokacin da wani baƙon zai zo bare ka san inda ya yi masauƙi.

Hausawa a wannan gari na Gombi sun zama kanwa uwar gami a kusan dukkan wani sha'ani na rayuwar yau da kullum, domin a ɓangaren da da ya shafi na shugabanci (sarauta) an samu Alh. Hamisu Abdullahi Majidaɗin gundumar Guyaku kuma sarkin babbar kasuwar garin Gombi da Alhaji Audu na Iro sarkin ayyukan gundumar Guyaku da Alhaji Yahya Yusuf Arabi Ubandoman gundumar Guyaku da Alhaji Yakubu Hamza Ajiyan gundumar Guyaku da Alhaji Bala Ammani sarkin Pawan gundumar Guyaku da Malam Magaji wakilin Hausawan gundumar Guyaku da Malam Hamza Maula sarkin Zango da Alhaji Sani Mumini sarkin Tasha da sauran masu unguwanni da dama (AlMusawi, 2022 da AlMusawi, 2024).

Sannan a ɓangaren siyasa Hausawa suna taka muhimmiyar a cikinta tun a jamhuriyya ta biyu, saboda an samu waɗanda suka zama shugabannin jam'iyyu kamar Malam Tanko makaniki shugaban jam'iyyar NEPU na ƙaramar hukumar Gombi da Alhaji Ado PRP shugaban jamiyyar PRP na ƙaramar hukumar Gombi da Alhaji Musale ya yi shugabancin jam'iyyar SDP na ƙaramar hukumar Gombi da Alhaji Malam mataimakin shugaban jam'iyyar NRC na ƙaramar hukumar Gombi da Alhaji Ɗalha Hassan shugaban matasan

6. Mal. Muhammadu Sa'adu (58) malamin addini an yi hira da shi (7:50am8:10am) ranar 12/09/2019 a ƙofar gidansa da ke Dadin kowa, Gombi.

jam'iyyar ACN na ƙaramar hukumar Gombi. Kuma an samu kansiloli cikin al'ummar Hausawa kamar Hon. Ibro Ammani (SDP) da Hon. Muhammad Shama (PDP) da Hon. Yusuf Musa Adamu (PDP).

Siyasar ƙaramar hukumar Gombi ba za ta cika ba, ba tare da ambato sunan Alhaji Yakubu Hamza ba. Wanda Bahaushe ne ya kuma riƙi kujerar shugabancin ƙaramar hukumar Gombi a ƙarƙashin jam'iyyar APC (AlMusawi, 2024).

Hausawa a garin Gombi duk da cewa ba 'yan asalin garin ba ne zuwa suka yi, mu'amalarsu da al'ummomin garin ta yi tasiri ga rayuwar al'ummomin a ɓangaren harshe, yanda kusan kowa yana amfani da harshen Hausa a matsayin harshen sadarwa tsakanin al'ummomin. Daga cikin gudummawar da Hausawa suka bayar ga garin Gombi har da yawan jama'a, domin yawan da Hausawa suke da shi ya taimaka wa yawan al'ummar garin. Sannan a fannin cimaka, al'ummomin garin sun riƙi abincin Hausawa kamar ɗanwake da waina da hura da nono da koko da ƙosai da ɗanbagalaje da kwaɗo da dambu da daƙuwa da alkaki da sauransu, kusan kowace al'umma a Gombi tana amfani da su. A gefen tufafi kuwa kai ka ce a wata alƙaryar ƙasar Hausa kake, domin al'ummomin garin suna amfani da tufafin Hausawa kamar shakwar da jamfa da wando da kaftani da sauransu. (Ladan & Al-Musawi, 2024).

A ɓangaren bayar da gudummawar ilimin addinin Islama kuwa Hausawa suna ajin gaba, domin kusan duk wata tsangaya fitacciya za a samu Bahaushe ne mai ita, misali daga cikinsu akwai: Alaramma Ɗan Amus na unguwar sabon layi da Sarkin malamai Atiku na unguwar NITEL da Alhaji Audu Bakatsine na unguwar Mayanka da Malam Abdullahi Ɗan baiwa na unguwar Clinic B. Sannan a makarantun Islamiyoyi kuwa akwai Islamiyyar Madrasatul Saƙafatul Islamiyya na unguwar shinge, akwai fitattun malamai a fannonin daban-daban kamar Malam Mukhtar Sa'adu Abdullahi da Malam Nura Abdullahi da Malam Abubakar Abdulrahman da dai sauransu. Sannan a fannin ilimin boko kuwa an samu Hausawa waɗanda suke riƙe da shaidar karatu a matakai daban-daban kamar *NCE* da *Diploma* da *Degree* da *Masters* a fannoni da yawa waɗanda ba za su lissafu ba. Sannan kuma suna aikin gwamnati a wurare mabambanta na daga koyarwa da ayyukan ofis-ofis (Ladan & AlMusawi, 2024).

### 2.5 Ra'in Bincike

An ɗora wannan binciken ne kan ra'in sauyesauyen al'adu (al'umma) wato Economic Theory of Social Changes, wanda Baturen Birtaniya mai suna Charlse Darwin (Feb. 12, 1809) ya ƙirƙira a shekarar 1859. Wannan ra'i yana bayani ne game da sauye-sauye da suke faruwa ga al'umma ko al'adunsu daga wani matsayi zuwa wani matsayi (Ado, 2017). Abin nufi ra'in yana wajjahar da hanyoyin da sassan turakun tattalin arziki suke sabbaba sauyesauyen tattalin arzikin al'umma, kamar sana'o'in kiwo da noma da sauran makamantansu. Sannan Gusau (2008), ya bayyana yanda al'umma takan fara tun daga gidan mutum ɗaya (mutum da matarsa). Daga nan sai muhalli ya koma gandu, daga nan sai ya koma tunga ta sana'a. Haka nan zai yi ta sauyawa ya koma unguwanni sai zuwa

ƙauye zuwa gari har ya ƙasaita ya koma birni. Sannan wannan sauyesauyen sukan shafi rayuwar al’umma a harkokin da suka danganci zamantakewar rayuwa da ƙungiyoyin da ke cikin al’umma na tattalin arziki da mulki… (Otite & Ogionwo, 1979). Kamar yadda gwagwarmayar Hausawa ta haifar da ci gaban al'ummomin garin Gombi. Sannan ta sanya su kan su Hausawan suka samu biyan buƙatarsu ta hanyar mallakar abin duniya.

### 3.0 Hanyoyin Tattara Bayanan Bincike

An nazarci ayyukan magabata na daga littattafai da kundayen bincike, an kuma tattauna da masana. Sannan an sanya idanu a kan lamuran rayuwar al'ummomi mazauna garin Gombi.

### 4.0 Tattalin Arzikin Hausawan Gombi

Tun da dai ana batun tattala dala ta koma sisi, a kuma yi tsimi da tanadin abin da ke hannu yau, domin ya bunƙasa ya kai gobe a wannan fannin Bahaushe yana ajin gaba. Kuma zai iya gwada tsayo da kowa a wannan ɓangaren a ra’ayin Bunza (2015).Wasu daga cikinsu ne suka samu wuri suka share a Gombi, saboda haka ba sai an faɗa ba, da yawa daga cikinsu sun zo ne da harkokin kasuwanci da ƙwadago da kuma sana’o’insu na gargajiya.

#### 4.0.1 Sana’o’in Gargajiya

Hausawan da suke zaune a Gombi sun riƙi sana’o’in da suka zo da su tun daga noma da kiwo da saƙa da rini da tsubbu da jima da ƙira da ɗinki da fawa da dukanci da wanzanci da sauransu, suka kuma ci gaba da rayuwarsu da wadannan sana'o'in.

#### 4.0.2 Kasuwanci Da Fatauci.

Haka nan wasu daga cikinsu suna yin nau’in kasuwanci na atai da jaura da ga ruwa da koli da kayan miya da arkomi da dillanci da magori da botori da sauransu, kuma ba su yi ƙasa a guiwa ba, sun ma faɗaɗa su ne.

#### 4.0.3 Kwadago

Haka aikin ƙwadago ma, ba a bar Hausawan a baya ba. Kwadago nau’in gyartai da saukale da roro da faskare da yanta da kitso da yankan farce da dakau da wanki da guga da dai sauransu, ga kuma uwa uba aikin gwamnati, wanda daga cikin Hausawa an samu masu aikin koyarwa da kuma aikin ofis a matakan ƙaramar hukuma da jiha da kuma na tarayya. Sannan a fannin siyasa ma akwai kansiloli da kuma shugabannin ƙaramar hukuma. Baya ga shugabannin ɓangarori da sashe-sashe a matakai dabandaban.

### 4.1 Sana’o’in Maza

Hausawan Gombi, musamman maza suna da sana’o’in da suka riƙa wanda shi ne hanyar ririta taro ya koma ɗari a gare su. Waɗannan nau’in sana’o’in sun haɗa da: wanzanci da tuƙi da kamasho da ɗori da gini da farauta da koli da fata da botori da aski da yankan farce da sauransu.

### 4.2 Sana’o’in Mata

Su kuwa matan Hausawan na Gombi suna da hanyar raya arzikinsu ta yin waɗannan sana’o’in waɗanda suka keɓance su ne, su kaɗai. Waɗannan sana’o’in sun haɗa da: koko da ƙosai da jaura da fura da masa da waina da ungozoma da ƙunshi (lalle) da kitso da dakau da sussuka da sauransu.

### 4.3 Sana'o'in Tarayya

Wannan nau'i na sana'a, ana samun maza da matan Hausawa suna aiwatar da su a Gombi, watau waɗannan sana'o'in an hadu a kai. Waɗannan sana'o'in kuwa su ne kamar: roron wake/gyaɗa da arkomi da Ɗinki musamman na jakunkuna ga mata da kiwo da noma da ƙwadago da dallaci da ginin tukwane da sauransu.

### 5.0 Sakamakon Bincike

Wannan bincike na tsokaci kan tattalin arzikin Hausawan garin Gombi; jiya da yau, ya gano waɗannan dalilai da suka sanya tattalin arziƙin Hausawan Gombi ya bunƙasa:

a) Kashin bayan tattalin arziƙin Hausawan garin Gombi ya dogara ne kan yadda Hausawan ba su bari wasu daga cikin sana'o'in gargajiya na gadon gidajensu suka mutu ba, dangin fatauci da kasuwanci.
b) Haka kuma akwai wasu nau'in sana'o'in da yawancin 'yan ƙasa ba su faye yinsu ba, misalin arkomi, musamman arkomin zamani (kasuwar buhu) wanda Hausawa suke hulɗa da Yarbawa da Inyamurai, yayin da ake tura musu (Yarbawa da Inyamurai) amfanin gona kamar gyaɗa da wake, su kuwa abokan kasuwacin (Hausawa) a turo mu su kuɗi ta banki.
c) Sana'o'in tarayya sun taimaka wurin raya tattalin arzikin Hausawa musamman a ɓangaren kiwon kifi da shanu da zomo da noman zamani kamar noman rani (Fadama I da II da III).
d) Daga cikin dalilan da suka raya tattalin arzikin Hausawan Gombi, har da zaƙewarsu wurin neman halal ganin cewa, nema ne ta kawo yawancin iyaye da kakanninsu Gombi. Saboda haka, ba su yi ƙasa a guiwa wurin sa himma ga hadafinsu ba.
e) Haka ma jajircewa da matan Hausawa suka yi a neman na kai musamman ta ɓangaren ungozoma da ƙunshi (lalle) da sauran ba da taimako na gyaran aure (maganin mata), sun taimaka gaya wurin raya tattalin arzikinsu.
f) Sannan sana'o'in mata irin na gida dangin ƙanƙara da yogurt sun kasance mataki na dogaro da kai, ba ga su matan kawai ba, har da mazan. Tun da kuɗin yana zagayawa ne tsakanin uwargida da maigida.
g) Wannan ƙumajin tattala arzikin ya haifar da duk mai sana'a yana ƙoƙarin ganin ya koya wa 'ya'yansa, domin ya rage zaman banza da kuma dogaro da kai.
h) Haka nan, binciken ya gano wata matsalar da wasu daga cikin Hausawan suke fuskanta, ita ce ta rashin wadataccen jari domin aiwatar da kasuwancinsu cikin nasara.
i) Sannan wani lokacin Hausawa suna fuskantar ƙyama daga wasu 'yan tsirarun al'ummomin garin da cewa su *warwardu* (baƙi) ne, wani zubin ma har hana su takardar shaidar zama ɗan gari *indigene letter* ake yi.
j) Har ila yau al'ummar Hausawan garin ba su da wata babbar hadaɗɗiyar ƙungiyar Hausawa mai magana da yawun duk Hausawan, sai dai wanda ba za a rasa ba, na daga ƙungiyar Hausawan da suka fito daga gari/jiha ɗaya (Kano ko Katsina ko Jigawa), ko ƙungiyar Hausawa masu wata sana'a iri ɗaya kamar mahauta da 'yan gwari da sauransu.

### 6.0 Shawarwari

Wannan takardar tana bai wa Hausawan garin Gombi shawara domin warware matsalar da suke fuskanta kamar haka:

i. Akwai buƙatar al'ummar Hausawan su kafa wata babbar ƙungiya wacce za ta zamo ta haɗe kan duk wata ƙungiyar Hausawan, domin ta zame musu mai magana da yawunsu.
ii. Haka nan, dole ne a samar da wata gidauniya wacce za ta riƙa samar da tallafi ga masu ƙaramin ƙarfi, ko kuwa ta riƙa bai wa masu ƙananan sana'o'i jari, saboda su faɗaɗa sana'o'insu har su bunƙasa.
iii. Sannan su ƙarfafi karatu musamman na zamani (boko), domin magance ƙyamar da ake musu ta hanyar amfani da karatun da suka yi. Saboda yin hakan zai wayar musu da kai cewa duk 'yan Nijeriya matsayinsa ɗaya ne, babu baƙo ba kuma ɗan gari duk Nijeriyawan ake.

## 7.0 Kammalawa

Ashe ba abin mamaki ba ne don an ga sabuwar motar alfarma ga Bahaushe ko shaƙaƙƙun shaguna (rumfuna) a bakin kasuwa ko kuma lambun zamani da makamakan gonaki mallakar Hausawa a Gombi. Duk sakamakon jajircewarsu ne, na tattala tare da more arzikin da Allah ya hore musu.

## Manazarta


AbuUbaida, S., Umar, B. & Ibrahim, M. (2019). Wanda ya tuna bara…Biɗa da tanadi a tsakanin Hausawa matasa a yau. Global Academic Journal of Humanities and Social Sciences, 2019. V0l.1, (2), (p4450). DOI:10.36348/gajhss.2019.v01i02.001

Adamu, A. U. (2020). Suna linzami: Hausa names as ethnographic identifiers. *Algaita: Journal of Current Research in Hausa Studies*. Bayero University, Kano. 13 (1), (p115).

Adamu, M.T. (1997). *Asalin Hausawa da harshensu*. Kano: Ɗan Sarkin Kura Publishers Limited.

Adamu, M. (1978). *The Hausa factor in West African history*. Zaria: ABU Press Limited.

AlMusawi, I. U. (2016). Teachers' qualifications and its effect towards the academic performance of Hausa students in some selected secondary schools. (B. A. Ed Project). Bayero University, Kano.

AlMusawi, I. U. (2022). Gudummawar matan Hausawa wurin bunƙasa tattalin arzikin garin Gombi na jihar Adamawa. *Proceedings: Women and their contribution to Hausa society*. In Haruon, H. K. and Aminu, N. (Editors). Kano: Versatile Educational Consultsncy Services Ltd (p220229). ISSN: 28113071.

AlMusawi, I. U. (2023). Nazarin kwatancin al'adun mutuwa tsakanin al'ummar Hausawa da ta Ga'anda. *Zaria Journal of Liberal Arts (ZAJOLA).* Vol. 11, No. 1, June 2023. (p8599). ISSN: 2141-3584.

AlMusawi, I. U. (2024). Gudummawar Hausawa ga cigaban garin Gombi a jihar Adamawa. *In Proceedings of the 3rd International Annual Conference on Science and Humanities: Bringing the Divide for Human Development (4th to 7th March. 2024).* Lafia: Federal University.

Auta, A. L. (2006). Tattalin arzikin Hausawa: Nazarin sana'a da kasuwancin Hausawa. *Algaita: Journal of Current Research in*

*Hausa*. V, DNL. Bayero University, Kano.

Bunza, A. M. (2015). Labarin zuciya a tambayi fuska: (Saƙon dariya ga sasanta tsaro a farfajiyar karatun Hausa). Takardar da aka gabatar a bukukuwan makon Hausa ta shekarar 2015 ta sashen nazarin harsunan Nijeriya. Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua. Katsina.

Bunza, A. M. (2017). *Dabarun bincike (Nazarin harshe da adabi da a'ladun Hausawa)*. Zaria: Ahmadu Bello University Press Ltd.

CNHN, (1981). *Rayuwar Hausawa*. Lagos: Thomas Nelson (Nigeria) Limited.

CNHN, (2006). *Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: ABU Press Limited.

Durumin Iya, M. A. (2006). *Tasirin kimiyya da ƙereƙeren zamani a kan sana'o'in Hausawa na gargajiya*. Kano: KABS Print Services (Nig).

Funtua, A. I. (2010). Ƙasar Hausa da yanayinta. *Al'adu da ɗabi'un Hausawa da Fulani*. Cikin S. M. Gusau & Funtua, A. I. (Editoci). Kaduna: ElAbbas Printers and Media Concept, (p1121).

Gwammaja, K. D. (2010). *Karin magana a ƙasar Hausa na II*. Kano: KDG Publishers Ltd.

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar al'ada da addini: Tasirin Musulunci kan rayuwar Hausawa ta gargajiya. (Kundin Digiri na Biyu). Jami'ar Bayero, Kano.

Ladan, S. & AlMusawi, I. U. (2024). Nazarin al'adun zamantakewar Hausawa da ta al'ummomin garin Gombi jihar Adamawa. *Jalingo Journal of Linguistics and Literary Studies (JAJOLLS)*. Vol. 8, No. 1, 2024. (p253260). ISSN: 24889067.

Maikwari, H. R. da Lawan, M. S. (2022). Gudummawar mata wurin bunƙasa tattalin arzikin ƙasar Hausa. *Proceedings: Women and their contribution to Hausa society*. In Haruon, H. K. and Aminu, N. (Editors). Kano: Versatile Educational Consultsncy Services Ltd (p229238). ISSN: 28113071.

Maiyaki, R. A. (2022). Bincike kan tasirin zamananci kan wasu sana'o'in matan Hausawa na gargajiya wajen bunƙasa tattalin arzikin al'ummar jihar Taraba. (Kundin Digiri na Biyu). Jami'ar Jihar Taraba, Jalingo.

NPC (2006). Population and Housing Census, result of Gombi Local Government Area.

Otite, O. & Ogionwo, W. (1979). An introduction to sociological studies. Heinemann (Nig) limited.

Umar, H. (2011). *Tattalin Arzikin Hausawa*. Katsina: Kanki Classical Media Enterprises.

*Vanguard Yellow Pages No. II* (1988).